# DEUTSCHE WELLE
# JI KI KARU

## Almara a Afirka domin al'adu da zaman lafiya:
## Bari na na ku labari
## Na takwas: Mujiya da Sarkin ƙwai


Wanda ya rubuta: Ibrahima Ndiaye

Waɗanda suka tace: Yann Durand, Stefanie Duckstein, Naïma Guira

Wanda ya fassara: Ɗanlami Bala Gwammaja


**'Yan wasa:**

Mai ba da labari

Sarkin ƙwai

Mujiya

Manyan dawa Zaki

MAI GABATARWA:

Masu sauraronmu, barkanmu da sake kasancewa da ku a cikin wani sabon shiri na “Ji Ki Karu” mai taken “Bari Na Ba ku Labari”. Kar ku manta, wannan shiri ne da ya ƙunshi hikayoyi na Afriki masu koya zamantakewa a tsakanin al’umma. Ina fata dai kowa kayansa a ɗaure yake, domin kuwa zan ɗauke mu ne cancak zuwa kan wani dutse da ke kusa da wani kogi, inda wata Mujiya ke zaune tare da Sarkin ƙwai. Sai ku ba mu aron kunnunwanku don ku ji yadda kowannensu ya samu kansa a cikin rikici, da kuma yadda kowa ya ƙwaci kansa. Don haka a gyara zama a saurari hikayar “Mujiya da Sarkin ƙwai”.

MAI BA DA LABARI:

Idan muki duba haka daga saman dutse, za mu iya ganin wani kogi a shimfiɗe kamar maciji. Ruwan wannan kogi dai garai-garai ne. Akwai bishiyoyi jere a kowane gefensa, kamar sojoji suna faretin ban-girma, ga waɗansu mutane da ke cikin wani kwale-kwale suna wucewa, waɗanda kuma suke ta ’yan waƙe-waƙensu ta hanyar bin kiɗan da sautin tuƙin nasu ke yi. To, a wannan wuri ne wata Mujiya da wani Sarkin ƙwai ke maƙwabtaki da juna.

Tun farkon fari dai, sun kasance suna jin daɗin wannan maƙwabtaka tasu, amma kuma bayan wani lokaci, sai Mujiya ta fara ƙosawa da irin surutun da maƙwabciyarta ke yi, wanda a kullum takan wuni tana waƙe-waƙe. Wata rana dai sai abin ya ishi Mujiya har ta nuna ƙorafinta cikin fushi:

MUJIYA:

“Don Allah wa ke mana wannan hayaniyar nan ne?”

SARKIN KWAI:

“Wallahi, ni ce nan Sarkin ƙwai, nake rera waƙa da muryata mai ɗaaaaan karen daɗi!”

MUJIYA:

"Wai ke don Allah ba za ki daina wannan waƙar ba ne? Yau fa satina uku ban yi barci ba saboda wannan muryar taki mara daɗi ta dame ni. Kuma… Kai! Bari ma dai na zo gaba da gaba na gaya miki!"

MAI BA DA LABARI:

Mujiya dai ta taso cikin fushi ta nufi wajen maƙwabciyarta mai takura mata.

MUJIYA:

"Abin da nake cewa shi ne, kina takura min da wannan ƙarar ɗin da kike yi. Yanzu har ta kai ina jin kamar na yi hauka."

SARKIN KWAI:

"Tsaya don Allah, Kaka Mujiya. Ni kuwa me na yi na ɓata miki?"

MUJIYA:

"Na ga alama nema kike ki mayar da ni abokiyar wasanki. Ki duba fa yadda nake ta faman neman abinci da daddare don na ci da iyalina, sannan kuma na huta da rana. To yanzu ga shi na zo nan don na samu na huta wa raina cikin kwanciyar hankali har ta Allah ta kasance, ban ga dalilin da zai sa yarinya kamarki ki dinga damuna ba. Don haka tun da dai ni ban dame ki ba, me ya sa don Allah kike wuni kina damuna da waƙe-waƙe?

SARKIN KWAI:

"Haba Kakata, ya kamata ki sani cewa ni fa mai ƙarfin imani ce. Da wannan waƙe-waƙe nawa nake shiga shauƙin yabon abin da nake bautawa. Kuma idan ba ki sani ba, wannan shi ake kira zikiri."

MUJIYA:

"To, ai ni ban san cewa zikiri kike yi ba. To na ji, bari ma dai mu yi magana a kan shi wannan addini naki. Ai dai a kowane addini akwai muhimman sharuɗa guda biyu, na girmama maƙwabci da kuma

haƙuri da juna, ko babu? Kin ga ke nan ya kamata ki dinga girmama ni. Idan kuma ma har yadda kike faɗa ɗin ne, cewa ke mai ƙarfin imani ne, me ta sa ba za ki gina wurin ibadarki ba ke kaɗai? Kin ga ma sai ki tara mabiya, ki zama mai wa'azi."

SARKIN KWAI :

"Ni fa Kaka, ba zan yi musu da ke ba. Amma ni bayanin da nake son na yi miki shi ne…"

MUJIYA:

"Ke, 'yar nan, ni yanzu maganar ta ishe ni! Na riga na gaji kuma barci neman kama ni yake. Idan kika yi tunani a kan sharuɗan nan na zaman lafiya da zamantakewa mai ɗorewa, to ki same ni."

MAI BA DA LABARI:

To yanzu dai Sarkin ƙwai ta zauna ita kaɗai tana tunanin maganar maƙwabciyarta. A kwana a tashi, sai Sarkin ƙwai ta fara nuna ɓacin ransa game da wannan al'amari, har ma ta fara gunaguni tana cewa:

SARKIN KWAI:

"Ni kuwa yaya zan zauna a rayuwata ba tare da na yi waƙa ba? Waƙa ai ita ce farin cikin rayuwata, kuma ita ce dalilin zamana a nan duniya. Ba zai taɓa yiwuwa ba a ce na yi wannan babban rashi don kawai na faranta wa wata tsohuwar tsuntsuwa mai mita! Ai ita ma ta san wasa take!"

MAI BA DA LABARI:

Sai kawai Sarkin ƙwai ta ci gaba da waƙe-waƙenta fiye ma da da. Sai dai kuma wani lokaci takan ji kunya idan ta tuno maganar da Mujiya ta yi mata.

SARKIN KWAI:

"Haƙiƙa bai dace a ce mutum ta kai waɗannan shekarun sannan a ce

ana damunsa ba. Gaskiya dai ya kamata a daina. Sai dai kuma me zan yi idan na daina waƙa? Gini zan koma yi, ko me? Yanzu wato sai dai na shafe rayuwata ina gina gidaje da sheƙar tsuntsaye da kuma kabarurruka ke nan? Kai, ina! Ai haka ma ba za ta yiwu ba, duk da dai na san abin da nake bai dace ba."

MAI BA DA LABARI:

A gaskiya Sarkin ƙwai ta ruɗe gaba ɗaya, don haka ma sai ta sake komawa wajen Mujiya:

SARKIN KWAI:

"Ni ce na sake dawowa, Kaka Mujiya. Na zo ne na faɗa miki cewa ba na son ki dinga fushi da ni, yadda har za mu daina magana da juna."

MUJIYA:

"Haba Sarkin ƙwai, mu daina magana da juna kuma? 'Yar nan, ai ni ban ma taɓa tunanin haka ba. Ni dai kawai cewa na yi ba zan dinga yi miki magana ba sai ran da ki daina son kanki. Kin ga wannan ai ya zama darasi a kanki. Yanzu ni ƙyale ni na yi barci, kya dawo wani lokacin."

MAI BA DA LABARI:

Daga nan sai Sarkin ƙwai ta yi tafiyarta cikin ɓacin rai a kan halayar da Mujiya ta nuna mata.

SARKIN KWAI:

"Kai, mutane da wuyar sha'ani suke. Idan dai suka yanke hukunci a kan wani abu, to ba abin da za ka iya yi a kai!"

MAI BA DA LABARI:

Sai Sarkin ƙwai ta yi ajiyar zuciya. Bayan ta koma gida, sai zazzaɓi ta rufe ta saboda ɓacin rai. Yanzu waƙe-waƙen ma da take yi sai suka zama rabi da rabi. Wasu lokutan ta yi, wasu lokutan ma sai ta shafe

kwanaki yi ba. Wannan hali da Sarkin ƙwai ta shiga ya jawo hankalin manyan dawa, wato Zaki. Ta kuwa lura da haka ne a lokacin da yake rangadin mataráutarsa don ya duba lafiyar talakawansa. A lokacin da ƙyar Sarkin ƙwai ta gai da shi, wanda hakan ya ɓata wa Zaki rai.

MANYAN DAWA ZAKI:

"Ke kuwa Sarkin ƙwai me yake damunki? Duk na gan ki a hargitse haka. Ko an yi miki rasuwa ne? Na san ke da yin waƙa, amma 'yan kwanakin nan sam ba ki yi."

MAI BA DA LABARI:

Daga nan sai Sarkin ƙwai ta yi wa Zaki bayanin matsalar da take ciki. Bayan da Zaki ya gama sauraronta, sai ya koma fadarsa ya kira taron dattawan masarautarsa, waɗanda suka haɗa da Giwa da Kunkuru da Akwiya da Zomo da kuma Hawainiya. Daga nan kuma sai suka aika Mujiya da Sarkin ƙwai su zo. Bayan an daɗe ana muhawara, sai Zaki ya karanta hukunci cikin muryar nan tasa mai kwarjini kamar haka:

MANYAN DAWA ZAKI:

"Mun tsaya a tsanaki mun yi nazarin wannan matsala da ta faru, kuma gaskiya yanke irin wannan hukunci ba abu ne mai sauƙi ba. Mun lura cewa ke Sarkin ƙwai ke kika san girman manya! Ke ce ki fara tunkarar Mujiya a kan wannan magana, domin ki nuna a shirye kike da a yi sulhu.
Ke kuma Mujiya, muna ganin ya kamata ki dinga ɗan kau da kanki idan Sarkin ƙwai tana waƙe-waƙenta. Ki sani cewa fa ita a yanzu kan ganiyarta take. Don haka muna so dukanku ku sani cewa, hanyar da za a fara warware kowace irin matsala ita ce, idan kana jin yadda wani yake ji."

MAI BA DA LABARI:

Da wannan bayani aka kammala taron, kowa ya koma gida. Wannan bayani na hikima da Zaki ya yi, ya kwantar wa da kowa hankali.

Yanzu dai Sarkin ƙwai ta koma yin waƙarta, amma fa yanzu tana taka-tsantsan, kuma waƙar yanzu tana daɗi ba kamar da ba. Yanzu idan Mujiya ta so yin barci, sai ta ɗan ƙara sama kaɗan a kan bishiya, inda muryar Sarkin ƙwai ta ɗan fi daɗin ji.
Hikayar tamu ke nan a yau! Duk wanda ya ji kuma ya yi amfani da darussan da ke ciki, to ba shakka shi ya rabauta.

MAI GABATARWA:
Duk da cewa Mujiya ba mai haƙuri ba ce, kuma shi ma Sarkin ƙwai takan cuskuna mata, amma kuma sun daidaita tsakaninsu sun zauna lafiya. To yanzu gare ku masu sauraro. Shin a shirye kuke koyaushe ku yi sulhu a tsakaninku idan wata matsala ta faru? Ta wace hanya kuke girmama wa sauran mutanen da kuke zaune da su? Yana da kyau ku je ku tambayi abokanku, sannan kuma ku tattauna wannan batu da magabatanku. Daga ƙarshe kuna iya rubuto ra'ayoyinku ko kuma abin da kuke zartar ta adireshinmu na yanar gizo, wato www.dw-world.de/lbe.